# الملاحق

## الملحق أ: أسئلة المقابلة

**<u>Tambayoyi game da yadda ake zartar da hukunchin yanke hannun Barawo a kotunan Muslumchi a arewachin Nigeria.</u>**

T1. Wadanne matakai ake bi don yin hukunchin sata?

T2. Wadanne Ka'idodi kuka shimfida kafin zartar da hukunchin muslumchi akan barawo?

T3. Shin ana bin dukkan abin da shari'ar muslumchi ta tanada wajen yanke hukunchin sata?

T4. Wanne iri tanadi kundin tsarin mullkin Kasa yayi kotunan muslumchi game da hukunchin sata?

T5. Shin akwai karo da juna tsakanin kundin tsarin mulkin kasa da shari'ar muslumchi game da hukunchin barawo? Idan akwai ta yaya ake maganche shi?

T6. Shin akwai wani tarki da kuke fuskanta ta bangaren siyasa game da zartar da hukunchin sata? Idan akwai ta yaya ake maganinsa?

T7. Shin yanayi na matsin tattalin arzikin kasa yana iya taka rawa wajen zartar da hukunchi akan barawo?

T8. Wadanne qalubale kuke samu wajen yanke hukunchin yanke hannun barawo?

T9. Shin akwai wasu matsaloli da kuke fuskanta game da kundin tsarin mulkin kasa ta yadda hakan yake zama takunkumi akanku wajen zartar da hukunchin sata?

T10. Shin akwai wani Kalubale da kuke samu ta bangaren sauran kotuna wadanda bana muslumchiba?

**الملحق ب**: القضية رقم C/NO. 71/2016 بين سليمان أديمولا وماريا إينيي

S/No: C/No.71/2016

S/Kotu: Sharia Court I T/Wada Zaria

Maisharia: Aminu Sa'adu Zarai

Maikara: Comm of Police KDS

Wanda ake Tuhuma: Idris Abubakar

Maigabatar da Kara: Sgt. Adamu Yahaya

Dalilin Kara: Shiga na Laifi da Sata Sections 118 da 139 SPC.

Ranar Sharia: 12/08/2016

Jawabin Mai gabatarwa

A ranar 11/08/16, da misalin karfe 10.45 na safe, wani Maisuna Suleman Ademola da Simon Maria Eneyi, sunzo atare charge office na Tudun Wada, Inda sukayi karan cewa a wannan ranar da misalin karfe 9.00 na safe, Maisuna Idris Abubakar, Banzazzau Zaria ya shiga masu gida ba tare da izininsuba, ya sace masu kayaiyaki kamar haka:-

(a) Generator Modern Sohu Tiger, 2700 mailaunin Kore, mai kimar N50,000.

(b) Gas cooker mai kalan lemu, mai kimar N8,500.00

(c) Riguna (2) masu kima N8,000.00

Jimla kimar ya kama N66,500.00 a yayin binciken 'Yansanda, an sami matahumi da dukkan kayan da aka lissafa, yin haka laifi ne da ya sabama tsarin laifuka da hukumcinsu na Jihar Kaduna a karkashin sashi na 118 dana 139 S.P.C.

Kotu ga Matahumi

Tambaya: Idris kaji tuhmar da ake maka, ka gane, ka yarda haka ne?

Amsa: Idris yace "naji na gane, kuma na yarda haka ne, na amsa.

Kotu ga Prosecutor

Tambaya: Prosecutor kaji matahumi yace, yaji ya gane kuma ya amsa laifinsa, me kace?

Amsa: Prosecutor yace " muna rokon Kotu da tayi masa hukumci atakaice (watau summary trial).

Samu da Laifi

- Bisa ikirari da kayi agaban Kotu na amsa laifin da ake tuhumarka akai, na shiga na laifi da yin sata, na sameka da laifi wadda zanyi maka hukumci atakaice.

Roko ko Hanzari

Tambaya: Kotu ga Matahumi – Idris kana da roko da zakayima wadda zatayi la'akari dashi tayi maka sassauci wajan hukumci?

Amsa: Idris yace " Ina dashi, saboda lallai nasan na amsa laifina don haka, ina roko Kotu tayi mani sauki da su kansu wadanda nayima satan.

Kotu ga Prosecutor

Tamabaya: Sagent, kaji rokon Matahumi ko kana da masaniya akan halin shi Matahumi?

Amsa: Sagent yace " wannan shine karo na farko agurinmu.

Horo.

Bisa la'akari da rokon da kayi ma Kotu, da bayanin da Prosecutor yayi agaban Kotu agame da cewa bai san halinkaba, wannan shine na farko agurinsu. Kotu ta horeka kai

Idris da biyan Tara na jimlar kudi N10,000.00 ko watanni (6 months) a gidan Yari.

Kuma zaka biya Diyyan wahalhalun kaiwa da komowa na kudi N2,000.00k

Daman Appeal.

Maikara ko Wanda ake kara, wadda bai yardaba, yana da daman ya daukaka kara zuwa gaba cikin kwanaki Talatin (30days) daga yau 12/08/2016.

(SGD) (AMINU SA'ADU ZARIA)
HON. AL-KALI
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA ZARIA.

CERTISFY TRUE COPY BY:-

(SAMAILA MOHAMMED)(ESQ)
ASST. CHIEF REGISTRAR
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA, ZARIA.

S/No. C/No.004/17

S/Kotu: Sharia Court I T/Wada Zaria

Maisharia: Aminu Sa'adu Zaria

Maikara: Comm of Police Kaduna State

W/ake kara: (1) Aliyu Sidi Aliyu

(2) Alhamid Ahmed

D/Kara: Shiga ta Laifi da Sata Sect. 181 da 139 SPC.

Maigabatarwa: Sgt. Adamu Yahaya

Lauyer Wanda ake tuhuma: Barr A.Y. Sambo

Jawabin Maigabatarwa

A ranar 12/01/17 da misalin karfe 4.30 pm. Wata Maisuna Jamila Yakubu. Mazaunin Sabon Layi Tudun Wada, Zaria yazo Police Station na Tudun Wada Zaria. Inda yayi karan:- Aliyu Sidi Aliyu da Alhamid Ahmad, da Ibrahim (Heras) mazauna Sabon Layi Tudun Wada, Zaria cewa a wannan rana da misalin 4.00 na yamma Mathumai sun hada kai sunyi shiga na laifi sun shiga shagonshi dake yankin da aka ambata sunansa a sama, (S/Layi) suka dauke mashi kayaiyaki kamar haka:-

- Card na Waya na layuyyuka dabam dabam, mai kimar N25,000.
- Kudi N30,000.00= Ayayin gudanar da Bincike, hukumar 'Yansanda Matahumai sun amsa laifinsu na aikata wannan laifin kuma suka ambaci akwai wadannan kaya sun dankasu a hannun Matahumi na uku (3) maisuna Heras, kuma ya gudu ana kan nemansa ne yanzu . yin haka laifi ne da ya sabama tsarin laifuka da hukumcinsu, a karkashin sashi na 181 da 139 SPC.

Kotu ga Matanumai na 1 da na 2.

Tambaya: Aliyu da Alhamidu, kunji tuhumar da 'Yansanda suke maku? kun gane, haka ne?

Amsa: Aliyu da Alhamidu sukace munji mngane, amma bah aka ba ne.

Kotu ga Prosecutor

Tambaya: Sargent, kaji suna musu, akwai sheda?

Amsa: Sargent yace "Muna da sheda, kuma muna rokonKotu ta bamu dama mu kawo shedu, sa'annan mu kamo mathumi na (3).

Kotu ga Lawyer Matahumi na 1 da na 2.

Tambaya: Barr. Me kukace?

Amsa: Barr. Yace tunda matahumai suna musu. Muna da roko a gaban Kotu Kotu shine ta badasu Matahumai beli bisa dogaro da sashi na 297 SCPC da kuma sashi na 36 karaman sashi na 5 da na 4 tare da Al-kawarra kamar haka:-

- Beli iko ne na Kotu, bisa Adalcin Shari'a da wannan muke rokon abada matahumai beli.
- In ambada belinsu, muna da tabbaci zasuyima Kotu biyaiya, kuma bazasu sake aikata laifiba. Ko makanta laifi a gaban wannan Kotu. Kuma ba zasy taba yin shishshigi don su lalata shariba, musamman tuhumar da ake masu.
- Kuma duk lokacin da aka kirasu Kotu zasuzo ba tare da bata lokaci ba.
- Don tabbatar da Adalci ga Matahumai in Kotu ta tashi bada beli, tasa matahumai akan sharudda masu sauki, saboda kowannen daga cikin matahumi yana da ruwa da tsaki akan tafiyar da harkan gidansu. Wannan shine rokommu, mun gode.

Kotu: Bisa dogaro da dalilai na sama, Kotu ta bada belin matahumai bisa tsabar kudi N25,000.00= ko Mashin rober – rober jincheng sabuwa zuwa ranar 23/01/17.

Dubi shafi (047).

23/01/17

Daga shafi na (038)

Comm.. of Police Vs. Sliyu Sidi & I Or.

Yau mai gabatar da kara Wakilin Comm. 'Yansanda Sargent Adamu Yahaya da Lauyer Barr. Y Sambo suna gaban Kotu don cigaba.

Kotu ga Prosecutor.

Tambaya: Sargent yaya maganar zuwa da shedu kun shirya?

Amsa: Sargent yace " kara ne ake masu na zargin Hada Kai, Shiga Na laifi da kuma sata, 181, 174, da kuma 139 SPC. Yau 23/01/17 ansa ne don fara sauraron shedu, kuma ashirye muke, muna da sheda guda (1) da zamu fara sauraron shedansa, in Kotu ta shirya.

Kotu ga shedan Maikara na (1)

| | |
|---|---|
| Suna: | Jamilu Yakubu |
| W/Zama: | Sabon Layi Tudun Wada Zaria |
| K/Hukuma: | Zaria Local Govt. |
| Sana'a: | Kasuwanci. |
| Shekaru: | (35 years). |
| Addini: | Musulnci. |

Al-kawali Sheda ya dauki al-kawalin fadin gaskiya agaban Kotu cewa " A ranar Alhamis da ta wuce 12/01/17 akwai inda su matahumai na 1 da na 2 suke taruwa suna kwallon tebur da 'yar zungure, sai sukazo dai – dai shagona, suka taru suna da yawa ni kuma ina gefen shagon sai Aliyu Sidi Matahumi na (1) ya fuskanci inda nake zaune, sai hankalina ya koma ina kallon kofar shagon, sai hankalina ya dan gushe kadan, nan take sai na shiga shagon, Allah ya taimakeni, sai na duba inda nake zuba Katin Waya

(Jaka) sai naga banga Katin dake cikin Jakamba da kuma kudi N33,000.00= Ina ganin banganiba, sai na sami shi Aliyu Sidin na kirashi gefe, na dunga rokonsa nace. Dun Allah wa kaga ya shiga mani shagon nan, cikin wadanda suke taruwa, tunda dama na ganshi yana haka da hannu, nace wannan bashi ne na dayaba, bashi ne na (2) ba, ka taimakeni ya nemo mani wadanda suke kwasan masa kaya, sai yace, sai nazo charge office nayi masu bayani. Da muka zo "Yan sanda suka fara yim masa tambayoyi, cewa, wa kasan ya shigam masa shago? Sai yace 'yasan wadanda suka shiga sune:-

- Matahumi na (2) Alhamid, da Ibrahim Moh'd. sai 'Yansanda sukace. Muje mu nemo Alhamid Matahumi na (2) da muka je bamu samshiba, sai yayansa yace, ai su Kotu zasu kawo maganar, saboda anyi ma

Kaninsu kazafin bata suna, a karshe "Yansanda suka kamoshi, a binciken da su kayi, sai Mathumi na (1) da na (2) suka cema "Yansanda da kudi da Kati yana gurin. Wanda ake tuhuma na (3) shine Ibrahim. Daga nan sai suka turo case din Kotu. Iya abinda na sani kenan.

Kotu ga Lauyer Wanda ake tuhuma na (1) da (2)

Tambaya: Barr. Kunji shedan Maikara na (1), kun yarda?

Amsa: Barr. Yace " munji, amma gaba daya bamu yarda da abinda ya fadiba, kuma muna da wasu "yan tambayoyi.

Lawyer Mathumai – Shedan Maikara na (1)

Tambaya: Jamilu Yakubu, ko zaka iya tunama Kotu kararrakin da kayi?

Amsa: Sheda yace. Kara ne na zargin Aliyu Sidi Aliyu na shiga shago da yin Sata.

Tambaya: Ka gayama Kotu, cewa yayin da kake zargin an shigan maka Shago, hankalin ka ya gushe, haka ne?

Amsa: Sheda yace " haka ne.

Tambaya: Idan mukace, tunda hankalinka yana gushe bazaka iya gane komaiba na abin da ka fadi haka ne?

Amsa: Sheda, yace, ba haka ba ne.

Tambaya: Tunda hankalinka ya gushe, amma ka iya gane abinda aka yi hakane?

Amsa: Sheda yace, ba haka bane.

Tambaya: Jamilu, alokacin da hankalinka ya gushe kaje ka kamo Matahumi na (1) ka kuma yi masa tambayoyi haka ne?

Amsa: Sheda yace ba haka ba ne.

Tambaya: Tunda kace, ba haka bane, idan nace, duk abinda ka fadama Kotu karya ne, nayi dai-dai?

Amsa: Sheda yace, bakayi dai – daiba.

Tambaya: Acikin shedanka, kace bayan hankalinka da ya dawo jikinka Ka fahimci ba Katin Waya, da kudi N33,000.00= a cikin jaka haka ne?

Amsa: Sheda yace, haka ne.

Tambaya: Amatsayinka na dan kasuwa, idan nace ka ruga police station ne, aka zo Kotu domin amayar maka da kudinka haka ne?

Amsa: Sheda yace, ey haka ne, su kawai nake nema.

Tambaya: Jamilu ko zaka iya fadama Kotu ko shekaranka nawa kana Kasuwanci?

Amsa: Sheda yace, sama da shekara (20years).

Tambaya: Zai kai shekara (25 years).

Amsa: Sheda yace, zai kai.

Tambaya: Jamilu kana da shekara nawa ka fara kasuwanci?

Amsa: Sheda yace, daga shekara (9) – (10 years).

Tambaya: Da kanka ka fara, ko kana karkashin wani ne?

Amsa: Sheda yace, ina karakashin Mahaifina ne.

Tambaya: A kasuwanci da ka shafe shekara (25 years) kana yi shi Matahumi na farko ya taba zama akarkashinka?

Amsa: Sheda yace, bai taba zamaba.

Tambaya: Akwai matsayi ka akeshi ya binciko maka wanda ya dauki Kaya?

Amsa: Sheda yace, nib a aikensa nayi ba.

Tambaya: Ka ganshi ne ya shiga shagon ko ko baka tabbatarda wanda ya shiga shagon ne ba, kakeso kaji daga gareshi?

Amsa: Sheda, yace ban tabbatar ko shi ne ya dauka, ko bashi ne ba. (Tambaoyimmu sun kare).

Kotu ga Prosecutor.

Tambaya: Sargent kuna da sauran shedu?

Amsa: Sargent yace " Muna da sauran shedu, amma muna da roko Shi ne Kotu ta bamu dama mu danyima shedan namu tambayoyi don mu sami yimma Kotu Karin hakikanin bayani mai ma'ana.

(Kotu ta ba ku).

Prosecutor – Shedan Maikara na (1)

Tambaya: Kace hankalinka ya gushe, kamar wani irin geshewa? (amma Lawyer yayi Objecting din wannan tambayan).

Kotu: Kotu ta dakata sai ranar 06/0217 don cigaba da jin shedun Maikara. Dubi shafi na (116).

21/03/17

Daga shafi na (47)

Comm of Police Vs. Aliyu Sidi Aliyu & 2 Ors.

Yau Matahumi (3) Ibrahim Mohammed yana Kotu da Lawyansa Barr. Maryam Muh'd. don cigaba, shi ne karantawa Matahumi na (3) tuhumar da ake masa.

Kotu ga Lawyer Matahumi na (3)

Tambaya: Barr. Kunce mene?

Amsa: Barr Maryam Muh'd. Ina tsayama matahumi na (3) Maisuna Ibrahim Muh'd. ansa yau ne don a karantama Matahumi na (3) Tuhumar da ake masa ka yarda haka ne?

Amsa: Ibrahim yace, naji na gane, amm ba haka bane.

Kotu – Prosecutor.

Tambaya: Sargent kaji matahumi na (3) bayan an karanta masa tuhumar da ake masa yace, yaji, ya gane, amma yana musu, akwai shedu?

Amasa: Prosecutor yace "Muna da cikakkun shedu da zamu gabatar a gaban Kotu da zamu tabbatar da ikirarn da mukayi ko kuma Da'awar mu na tuhumar da muke dashi. Kuma muna rokon Kotu da ta bamu wata rana don mugabatar da cikakkun shedummu.

Kotu – Lawyer Matahumi na (3)

Tambaya: Barr kinji, me zakice?

Amsa: Barr tace, naji, Allah ya kaimu. Sai dai ina da roko, shi ne adawo mana da sheda na farko, don muyi masa tambayoyi, saboda bamu yi masa tambayoyin ba.

Dubi shafii na (120).

05/04/17

Daga shafi na (116)

Comm of Police Vs. Aliyu Sidi Aliyu & 2 Ors.

Yau mai gabatar da kara Sargent Adamu Yahaya da Mathumi (3) da Lawyer Mai tsayama Matahumi na (3) suna gaban Kotu don cigaba.

Kotu ga Sargent.

Tambaya: Sargent ina aka kwana ne bisa kan wannan shari'a?

Amsa: Sargent yace, an sanya sharian ne zuwa yau, don cigaba da jin Shedummu kuma a shirye muke.

Kotu ga Shedan Maikara na (2)

| | |
|---|---|
| Suna: | Abdullahi Isa |
| W/Zama: | Chikaji Sabon Gari, Zaria |
| K/Hukuma: | S/Gari Local Government |
| Sana'a: | Dan Sanda |
| Shekaru: | (33 years) |
| Addini: | Musulunci. |

Al-kawari sheda ya dauki al-kawarin fadin gaskiya agaban Kotu cewa " zan iya tuna cewa ranar 12/01/17, Ina bakin aiki a nan Tudun Wada Police – Station, amatsayin Dansanda mai bincike, wani Bawan Allah, maisuna Jamilu yazo da korafin cewa yana da shago a Sabon Layi, na saye da sayarwa, a wannan rana da na fadi yana bakin kasuwancinsa, akwai sunuka, anayi kusa da shagon nasa, yace, ba sau dayaba, ba biyuba, in Yaran nan sun taru, sun rufe masa shago, in yace su tashi, sai abin ya zama masu fitina, awannan rana, say ace akwai wasu Yara matasa, kamar Aliyu Sidi, da Alhamid da wasu kuma da bazai iya fadin sunayensu ba, sai fita ta kamashi da makwabcinsa da ke kusa da shagonsa acewarsa, bai wuce minti (15 ba) sai hankalinsa ya komo zuwa ga shagonsa, acewarsa akwai kudi N32,000.00= a shagon da recharge cards na network iri – iri a shagon, na zallar kudi N25,000.00= da yazo ya binciki wadannan kaya, yaga babu, sai ya garzayo zuwa Kotu a

sakamakon haka ne, ya fada mana wadanda yake zargi, sai muka jagoranci bincike, inda muka samo Aliyu Sidi mukayi amfani da Damammaki irin tamu ta dibaru don tabbatar da laifi ya tabbata ko bai tabbata ba, sai Aliyu Sidi bai wahalar da sharia ba, yace lallai wannan laifi ya tabbata, shine ya ambaci Alhamid (Matahumi na (2) bayan zuwan Alhamid, sai shima ya tabbatar da hakan, amma yace, da kudi da recharge card, duk sun tattara sumba shi matahumi na (3) Ibrahim. Sai muka baza kamar neman matahumi na (3) amma bamu sameshiba, yayi mana batar dabo, muna tsakiyar bincike, sai wani dan'uwan Alha mid yazo ya bukaci ganin dan'uwansa sai na kirashi, ~~nayi~~ naji yana tambayarsa ka amsa, yace, ey sai yace masa damme zaka ansa, wa yace ka amsa ni dai ban san sunansa ba, ganin yadda abin take, shi ne muka kawo case din Kotu, iya abind na sani kenan.

Kotu ga Lawyer Matahumi na (3)

Tambaya: Barr. Maryam, kinji shedan Maikara na (2) kun yarda?

Amsa: Barr tace "munji bamu yarda ba, amma muna da tambayoyi.

Lawyer Matahumi na (3) – Shedan Maikara na (2)

Tambaya: Aliyu Sidi ya kwana a Station kafin ya amsa, tuhumar da ake masa hakane ko bah aka ba ne?

Amsa: Sheda yace, ba haka ba ne.

Tambaya: Statement din sa, shi ya rubuta, ko yana fadi ne ana rubutawa?

Amsa: Sheda yace, yana fadi ne ana rubuta wa.

Tambaya: Shi steps din nan guda (6) na Police Acts, kayi amfani dasu Daya bayan daya, ey ko a'a?

Amsa: Sheda yace "nayi".

Tambaya: Kace matasa da yawa suna taruwa, a wurin haka ne?

Amsa: Sheda yace, kwarai kuwa.

Tambaya: Zan iya cewa su matahumai daga cikin matasan nan da yawa aka tsamosu haka ne?

Amsa: Sheda yace, haka ne.

Tambaya: Akwai sanaiya kenan, tsakanin matasa das hi mai shagon, haka ne?

Amsa: Sheda yace, ey haka ne.

Tambaya: Sauran matasan da ba'a sansuba, saboda su wadannan an Sansune, shi yasa aka tsamosu, haka ne?

Amsa: Sheda yace, hakane.

Tambaya: Shi mai shagon a Minti (15) da yayi baya kallon shagon, don haka, bai san wadda ya shigaba, bai san wadda yafita ba, haka ne?

amsa: Sheda yace, hakane.

Tambaya: Doka ta baku dama ne wajan bincike ku bugi mai laifi, ko ku Yaudareshi ko agabatar dashi a yayin tuhuma?

Amsa: Sheda, yace, ey ta bamu dama.

(Tambayoyimmu sun kare)

Kotu ga Sargent

Tambaya: Sargent, kuna da sauran shedu?

Amsa: Sargent, yace" muna dashi, sai dai abamu wata rana.

Kotu: Kotu ta dakata sai ranar 12/04/17.

Don cigaba da jin shedun Maikara.

Dubi shafi na (130).

28/04/17

Daga shafi na (120)

C/No.004/17

Comm. of Police Vs. Aliyu Sidi & 2 Ors.

Yau Mai gabatar da kara, Sargent Adamu Yahaya, da Matahumai (3) da Lawyer mai tsayama Wanda akai kara Barr. Maryam Muh'd. suna gaban Kotu don cigaba da jin shedun Maikara.

Kotu ga Sargent.

Tambaya: Sargent, kunzo da sauran shedun naku yau, ko baku shiryaba?

Amsa: Sargent yace " a shirye muke da mu rufe case dimmu, saboda Shedan mu da zamu kawo, yayi tafiya zuwa Kasan Waje, don haka a shirye muke mu rufe case dimmu yau.

Kotu ga Lawyer Matahumai

Tambaya: Barr kinji, shedansu yayi tafiya zuwa waje, don haka, zasu Rufe case dinsu yau, kuma a shiye suke, kufa?

Amsa: Barr tace, tunda haka ne, muna rokon Kotu ta bamu date don mu bude Defence dimmu.

Kotu: Kasancewar masu gabatar da kara sunce yau ne zasu kawo shedansu na karshe, amma kuma sunce zasu rufe case dinsu yau, maganar sheda shikenan, sai dai Kotu bata saniba rufe din na jin shedunne ko nawani abu ne, ala ayyi halin Kotu ta amince masu da rokonsu.

Kotu ga Sargent

Tambaya: Sargent Bisillilla, kan maganne ku na rufe case.

Amsa: Sargent yace. Muna rokon Kotu ta bamu wata rana.

Kotu ga Lawyer Matahumai.

Tambaya: Barr kinji sun rufe case dinsu, me zakuce ku kuma?

Amsa: Barr, tace "Muna rokon Kotu ne dama ta bamu, wata rana don Mu bude Defence dimmu.

Kotu:

Kotu taji rokon ku, kuma ta amince don haka, ta baku ranar 08/05/17 don kuzo ku bude Defence dinku, ko ruling din Kotu.

Dubi shafi na (155).

19/05/17

Daga shafi na (130) C/No.004/17

Comm of Police Vs. Aliyu Sidi & 2 Ors.

Yau mai gabatar da kara Sargent Adamu Yahaya da Matahumai guda (3) da Lawyer mai tsayama Matahumi suna gaban Kotu don cigaba, shine shawaran Kotu.

Shawaran Kotu:

Kotu taga wannan kara da Comm of Police na Jihar Kaduna ya shigar agaban wannan Kotu, Inda yake tuhumar Aliyu Sidi Aliyu, da Alhamid Ahmad da Ibrahim Muhammad da shiga na laifi da yin sata, a karkashin sashi na 181 da 139 SPC.

Ajawabinsa na gabatar da kara, wadda Kotu ta fara saurare a ranar 16/01/17, Dan sanda mai gabatar da kara, Sargent Adamu Yahaya cewa yayi " wani maisuna Jamilu Yakubu yazo Ofishin 'YanSanda na Tudun Wada , Zaria Inda yayi karam Matahumai abisa kan cewa ranar 12/01/17, da misalin karfe 4.30 na yamma shi Jamilu Yakubu ya fada masu cewa Matahumai (3) sun hada kai, Inda suka yi shigo na laifi a shagonsa, suke dauke masa katin waya mai kimar kudi N25,000.00= da tsabar kudi N30,000.00= inda mai gabatar da kara yace, a yayin bincike, Matahumai sun amsa laifinsu, amma sukace wadannan kayaiyaki suna hannun Matahumi na (3) Maisuna Ibrahim Muhammed wato (heros). Da Kotu ta waiwayi Matahumai sai suka ce " suna musu, sai Kotu ta bada belinsu ta bukaci mai gabatar da kara da sukawo shedu, inda suka gabatar da mutum (2):-

- Jamilu Yakubu, dan shekara (35 years) Mazaunin Sabon – Layi, Dan Kasuwa Musulmi, bayan ya dauki al-kawarin fadin gaskiya agaban

Kotu, sai yace, Mathumi na (1) da na (2) suna kusa da shagonsa suna wasan 'yar zungure, kuma suna da yawa, yace, shi kuma yana kusa da shagon a gefe daya, sai Matahumi na (1) Aliyu ya fuskanci inda shi sheda yake zaune sai hankalin sheda na (1) ya koma inda ake wasan kwallo, daga nan sai da ya farga, sai ya shiga shagon shi ne sai ya Ankara cewa an shigam masa an satan masa kudi N30,000.00 da carda na wata mai kimar N25,000.00 amma bai san ko waye ya shigaba, dalili yace ma matahumi na (1) Dun Allah wa kaga ya shigam mani shagon nan, cikin wadanda ke taruwa ana nan suna wasa? Yace yaga Aliyu yana haka da hannu, sheda yace bashi ne na dayaba ba shi ne na (2) ba.

Kotu bata amshi wannan shedam ba saboda dalilai kamar haka:-

(1) Akwai zato ga sheda na (1) don yace ma Aliyu wane kaga ya shigam mani shagon nan.

(2)Shi kansa shaida bai fahimci an shigam masa shagoba, sai bayan ya koma cikin shagon.

(3)A shari'ar Musulunci Kotu ba ta aiki da zato sai hakika, shi ko sheda zato yakeyi bashi da tabbatas.

Sai sheda na (2) Maisuna Abdullahi Musa, Mazaunin Chikaji Sabon Gari Zaria, dan shekara (33yrs) kuma Dan Sanda mai bincike, Musulmi, bayan ya dauki al-kawarin fadin gaskiya agaban Kotu, sai yace, sheda na (1) Jamilu Yakubu yazo ofishinsu inda yayi masu bayanin cewa Matahumi na (1) da na (2) sun shigammasa shagonsa sunyi masa satan Katin waya mai kimar kudi N25,000.00= da kuma kudi N33,000.00= amma yace Matahumai (2) sun fada masa kayan suna hannun Matahumi na (3) ne daga nan ya zaiyana yadda sukayi

da Matahumai. Dubi shafi na (120 – 122). Na wannan littafi. Shima Kotu bata amshi shedarsaba saboda.

- A Shari'ar Musulunci, Maikara baya sheda da kansa , koma wani irin karane, sai dai ya kawo shedu in sun tabbata a hukumta matahumai. In kuma basu tabbataba a sallami, karan da Wanda ake kara. Saboda hujjar da Manzon Allah yake cewa:-

..........................................................................................

Ma'ana: sheda tana kan Mai Da'awa rantsuwa ke kan mai musu take. Sai dai a tsarin Musulunci dai har wa yau, a irin wannan tuhuma ba'asa mutum ya rantse sai dai rantsuwar tuhuma kamar yadda mai tuhufa yace cewa:-

..........................................................................................

..........................................................................................

Ma'ana, Ita rantsuwa ta tuhuma in tuhumar tayi karfi sosai to Matahumi wajibine ya rantse cewa, bai aikata wannan laifi da ake tuhumarsa akai ba. Kuma ba'a juyar da ita (ma'ana baza a koma da rantsuwarn ga Maikara ba don ya rantse, in Wanda ake kara yaki yarda ya rantse.

Bisa dogaro da wadannan dalilai, Kotu ta dage cigaba da sauraran shari'ar sai zuwa ranar 26/05/17, don yin shawara gas u Matahumai (3) na yin rantsuwa, ko rashin rantsuwan saboda Kotu ta fahimci tuhumar tayi karfi bisa dalilai kamar haka:-

- Matahumi na (1) da na (2) sunyi ikirari agaban charge office cewa kaya yana hannun matahumi na (3) Ibrahim Muhammad. Shi kuma yayi musu. Kaga jayaiyyan matahumi na (1) da na (2) da shi na (3) kamar yana karfafa tuhumar da ake masu ne.
- Sheda na (1) yace, yaga matahumi na (1).

Dubi shafi na (202).

07/07/17

Daga shafi na (155)

C/No.004/17

Comm. of Police Vs. Aliyu Sidi & 2 Ors.

(SGD) ( AMINU SA'ADU ZARIA)
THE HON JUDGE
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA ZARIA

CERTISFY TRUE COPY BY:-

(SAMA'ILA MOHAMMED) (ESQ)
ASST.CHIEF REGISTRAR
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA, ZARIA.

**الملحق د**: القضية رقم C/No.50/16

S/No. 150/16 C/No.50/16

S/Kotu: Shari'a Court Tudun Wada, Zaria

Maisharia: Aminu Sa'adu Zaria

Maikara: Comm. of Police KDS

Mathumai: (1) Abubakar Muhammad

(2) Zubairu Aliyu

Dalilin Kara: Hada kai da Sata, Sec, 118 & 139 SPC.

Maigabatarwa: Sgt. Adamu Yahaya

Ranar sharia: 30/06/16

Jawabin Maigabatarwa

A ranar 29/06/16, da misalin karfe 8.00 na safe, wani maisuna AlRahman Isah, mazaunin layin Rimi Tudun Wada, Zaria yazo Police Station na Tudun Wada. Inda yayi karan mathuman abisa kasancewa sun haka kai tare, sun kwace N450.00 a hannunsa Dansa Maisuna A/Rahman,a yayin binciken 'Yan sanda, Mathumai sun amsa laifin da ake tuhumansu akai, amma sunba jinjiri ne kudin. Kuma ya gudu, ahalin yanzu ana nemansa ne kuma halayensune su kwace ma mutane kudi ko waya daga nan har zuwa cikin Zaria. Kuma akwai sauran kamar Abu da Umar da Kabiru da Falalu, har yanzu suma ana neman sune, saboda ba'a gano Iyayensuba. Wannan

shine bayanimmu, kuma yin haka, laifine da ya sabama tsarin laifuka da hukumcinsu na Jihar Kaduna.

Kotu ga ~~Mata~~ Matahumi na (1) da na (2)

Tambaya: Abubakar da Zubairu, kunji tuhumar da ake maku, kun gane, kun yarda hakane?

Amsa: Dukansu sukace "Munji mun gane kuma haka ne ya maigirma ya Maisharia.

Kotu ga Prosecutor:

Tambaya: Sgt. Kaji sun amsa laifunsu, me zakace?

Amsa: Sgt yace "Muna rokon Kotu tayi masu hukumci atakaice (summary trial).

Kuma tayi masu umarni da su biya Maikara kudinsa N450.00

Samu da Laifi

Kotu ta sameka kai Abubakar da kai Zubairu da laifin da ake tuhumarku akai sakamakon ikirarin da kukayi a gaban Kotu, da bakinku ba tare da Kotu ta turssamakuba, don haka< Kotu zata hukumtaku dai-dai da laifinku, saboda Annabi )S.A.W.) yace:-

.......................................................................................................

Ma'ana:- yin ikirari yafi zuwa da shedu".

Kotu ga Mathumai na (1) da na (2)

Tambaya: Abubakar da Zubairu, ko kuna da rokon da zakuyima Kotu tayi maku sassauci wajan hukumci?

Amsa: Sukace "Muna rokon Kotu tayi mana afuwa, In sha Allahu daga wannan bazamu kara ba, Abubakar yace mu (2) ne ake cema, tozo, shi Zubairu Wanda ake kara na (2) shine ya dauki kudin da shi da wannan tozon, ,amman ni ina kasuwane, aka zo aka kamani. Shi Zubairu ya tabbatar cewa ba wannan Abubakar din bane, kamar yadda Abubakar din ya fadi.

Kotu ga Prosecutor.

Tambaya: Sgt, kaji hanzarinsu, ko ka taba samunsu da irin laifi Makamancin su?

Amsa: Sgt. Yace a'a ban taba samuba.

Horo

Kotu ta sallameka kai Abubakar saboda kasancewar Wanda ake kara na (2) Zubairu ya tabbatar da cewa bakai ake nufiba, amma tunda an tuhumeka, ka amsa cewa, hakane, Kotu zata horeka da bulala (7) da taran N500.00 ko sati (2) a gidan Yari. Kai kuma Zubairu tunda kaine

ummul'aba'is na laifin, kuma ka amsa, Kotu ta horeka da biyan tara na kudi N2,000.00 ko watanni (2) a gidan Yari, tare da bulala (12) amatsayin Ta'azir.

Daman Appeal

Maikara ko Wanda ake kara wanda bai yardaba, yana iya daukaka kara zua USC cikin kwanaki Talatin (30days) daga yau 30/06/16.

(SGD) (AMINU SA'ADU ZARIA)
HON. AL-KALI
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA, ZARIA

CERTISFY TRUE COPY BY:-

(SAMAILA MOHAMMED)(ESQ)
ASST. CHIEF REGISTRAR
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA, ZARIA.

**الملحق هـ**: القضية رقم C/No.008/16

S/No.19/16 C/No.008/16

| | |
|---|---|
| S/Kotu: | Sharia Court I T/Wada, Zaria |
| Maisharia: | Aminu Sa'adu Zaria |
| Maikara: | C. of Police KDS. |
| Matahumi: | Mustapha Haruna S/Gari, Zaria |
| D/Kara: | Shiga na laifi da Sata Sect. 174 & 189 SPC. |
| Mai Gabatarwa: | Cpl. Adamu Yahaya |
| R/Sharia: | 19/02/16 |

Jawabin Maikara

Amadadin Comm of Police na Jihar Kaduna, ni Mai No. 252850, Cpl, Adamu Yahaya ina gabatar da Matahumi Mustapha Haruna abisa kan cewa, ranar 17/02/16, da misalin karfe 8.00 am wani Maisuna ~~Kamauddeen~~ Kamaluddeen Aliy, mazaunin Sabon Layi Tudun Wada yazo Ofishin 'Yansanda na nan Tudun Wada inda yayi karan cewa wani Maisuna Mustaha Haruna, mazaunin Sabon Gari Zaria, cewa a wannan rana, shi Matahumi yayi masa shiga ta ~~lafi~~ laifi a Dakinsa inda ya dauke masa waya Tecno, mai kimar N4,500.00 ya kuma dauke masa waya kirar Nokia, mai kimar N1,500. Sai karamar jaka mai dauke da 18 card na wurin aikin Maikara da A.T.M. (2) da Katin Zabe, a yayin da aka kama shi Matahumi an sameshi da waya kiran Tecno, wadda mallaki ne na Maikara. Inda ya dauka babu izini, yin haka, laifi ne day a sabama tsarin laifuka da hukumcinsu na Jihar Kaduna SPC. Wannan shine bayanimmu.

Kotu ga Matahumi

Tambaya: Mustapha Haruna kaji tuhumar da ake maka, ka gane, ~~kai~~ ka yarda ka amsa Laifinka, ko kana da ja?

Amsa: Mustapha yace “naji na gane kuma rankai dade na amsa.

Kotu ga Prosecutor

Tambaya: Cpl. Kaji matahumi ya amsa laifinsa, dudda haka, kana da sheda, ko kun gamsu da ikirarinsa?

Amsa: Cpl. Yace “ muna da sheda, amma tunda ya amsa bamu da wani bukatar mu gabatar da sheda akai dama yana musu ne, sai mugabatar da shedummu.

Samu da Laifi.

Bisa ikrari da Matahumi yayi agaban Kotu, ba tare da an tursasashi ba, Kotu ta sameshi da laifi na shiga ta laifi, da sata akarkashin sashi na 174 da 139 SPC. Don haka Ktu zata yanke maka hukumci.

Kotu ga Matahumi

Tambaya: Kafina Kotu tayi maka, hukumci, ko kana da roko da zakayi ma Kotu da zaisa tayi maka sauki?

Amsa: Matahumi yace “ ey akwai, na farko dai ina da sana’a ba zaman banza nake yiba. Kuma nayi al-kawarin bazan sake daukan kayan waniba. Ina zaune a garin nan akarkashin Malam Yahaya, (Kakanane), amma ya rasu daga nan nema na koma sana’ar tura baro, sai kuma na koma sana’ar shoe shainer (wankin takalma) kuma mahaifiyata ta rasu, ni nake nemama kaina abinci wannan shi ne rokona.

Kotu ga Prosecutor

Tambaya: Cpl, Adamu, kaji rokonsa, kafin Kotu tayi la’akari da rokonsa, ko kun taba Samunsa da laifi makamancin haka?

Amsa: Prosecutor yace, bamu taba samunsa ba, sai dai akwai alamun ya saba, sai, dai abinda Kotu kuma tayi.

Horo:

Bisa la'akari da rokon da kayima Kotu na tayi maka sauki, da ikirarin da kayi agaban Kotu, ba tare da ka wahalar da sharia ba, ni Maisharia Aminu Sa'adu Zaria, na koreka kai Mustapha Haruna da biyan tara na kudi N3,500.00 ko daurin watanni uku (3) agidan Yari, kuma zaka biya diyyan waya kirar Nokia N1,500.00. jimla zaka biya N5,000.00 kenan.

(SGD) (AMINU SA'ADU ZARIA)
THE HON. AL-KALI
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA, ZARIA

CERTISFY TRUE COPY BY:-

(SAMAILA MOHAMMED)(ESQ)
ASST. CHIEF REGISTRAR
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA, ZARIA.

S/No. C/No.18/2017

S/Kotu: Sharia Court I T/Wada Zaria

Maishari'a: Aminu Sa'adu Zaria

Maikara: Comm of Police Kaduna State

Matahumai: (1) Sa'idu Shehu T/Jukun Zaria

(2) Sani Sa'adi T/Jukun Zaria

(3) Salihu Ladan T/Jukun Zaria

(5) Adamu Kabiru T/Jukun Zaria

Dalilin Kara: Criminal) Hada kai, Sata, Siyen Kayan Sata Sext. 117 da 139 SPC.

Ranar Sharia: 10/07/17

Jawabin Mai Gabatar da Kara.

Tambaya: Seargent mene karanku?

Amsa: sergent yace sunana Sergent Adamu Yahaya, ina gabatar da Matahumai abisa kan cewa a ranar 06/07/17, da misalin karfe 10.30 na safe, wata Maisuna Nafida Yakubu mazauniyar Tudun Jukun Zaria tazo Ofishin 'Yansanda na Tudun Wada Zaria inda tayi karan matahumai cewa a ranar 05/07/17, da misalin karfe 2.00 na rana su matahumai da aka ambata sunayensu a sama, sun hada kai na laifi, inda suka dauke mata Akuyarta, suka tafi da ita ba tare da izinintaba, mai kimar kudi N10,000.00 suka yankata, sai jama'ar Unguwa, tare da Hukumar 'Yansanda suka hadu suka tafi suka kamosu suka gabatar da su wajan Hukumar 'Yansanda don yin bincike akansu. Kuma sun tabbatarda aikata wannan laifi a yayin bincike, kuma sun saidama Maisuna Adamu Kabiru Matahumi na (4). Wannan laifi ne da ya sabama tsarin laifuka da Hukuncinsu na Kasa sashi na 117 da 139 SPC.

Kotu ga Matahumi na 1 – 3:

Tambaya: Sa'diu, Sani, Salisu kunji tuhumar da ake maku, kun gane, kun yarda da haka ne?

amsa: Gaba dayansu su (3) sukace "ey, munji, mun gane, kuma haka ne mun amsa laifimmu.

Kotu ga Matahumi na (4).

Tambaya: Adamu kaji kai abinda ake tuhumarka, akai, na siyan kayan sata ka gane, ka yarda haka ne?

amsa: Adamu yace "naji, na gane, kuma haka ne.

kotu ga Sergent.

Tambaya: Sergent kaji matahumai na 1 – 3 sun yarda da tuhumar da ake masu na shiga ta laifi tare da aikata sata, haka shima Mai saye, ya yarda ya amsa nasa laifin na siyan kayan sata me zakace?

Amsa: Sargent yace " muna rokon Kotu da tayi ma kowannensu Hukumci a nan take (wato summary trial) tare da sasu su biya Diyyan wannan Akuya na kudi N10,000.00= sakamakon Ikirari da sukayi agaban Kotu ba tare da tursassawa koannn suba.

Kuma ance:-

"الإقرار أولى من الشهود"

Ma'ana " yin ikirari, yafi zuwa da shedu"

Samu da laifi

Kotu ta sami kowannenku da laifi sakamakon yin ikirari da kukayi agaban Kotu cikin hankalinku, kuma ba tare da an tursasa makuba, don yanzuKotu zata yi maku hukumcin da ya dace daku.

Uzuri: الإعذار

Kotu kafin Kotu tayi maku hokum ci, dudda kun ansa laifinku, Kotu zataso taji hanzarinku. In kuna dashi ko rokon da zaisa Kotu tayi maku sassauci wajen wajan hukumci?

Kotu – ga Matahumai na 1 – 3

Tambaya: Sa'idu ko kana da wani hanzari ko roko da zakayima Kotu, kafin tayi maka hukumci?

Amsa: Sa'idu yace " ni kadai ne baba awajan Mahaifina, kuma bani da Kudin da zambiya kudin jarabawa na Makaranta, babana ya gaza da farko ya bani, sai kudin suka zube, Ina jon tsoron in koma mai kada yace karya nakeyi.

Tambaya: Kaifa Sani?

Amsa: Sani yace " ba abinda zance, sai nasan na aikata kuskure, nabi, son zuciya, in Allah ya yarda nayi alkawari bazan sakeba.

Tambaya: Kai kuma fa Salisu?

Amsa: Salisu yace " ai tsautsayi ne.

Kotu ga Matahumi na (4)

Tambaya: Kai kuma fa mai sayen kayan sata wani roko zakayima Kotu?

Amsa: Adamu yace " wannan abu da na aikata, har ga Allah ba laifina ba ne; kuskure ne, ni har gida aka kawo mani, amma ba sana'ana bane, naje na siya agidansu, kuma zanyi tsammanin nasu ne ba na sata bane. Kuma ban sansu da sata ba.

Kotu ga Sargent.

Tambaya: Sargent, kaji uzurin kowannensu ko me zakace abisa kan Halayensu, ko an taba gabatar da dayansu gabanku?

Amsa: Sargent yace " lallai lafi ne da suka saba aikatawa, Mutane da dama suna ta zuwa, suna cewa " yanzu haka sune suka yanka masu Awakansu.

Kotu:

Bisa dogaro da ikirarin da Matuhumi na 1 da na 2 na 3 sukayi, agaban Kotu, ni Maishari"a Aminu Sa'adu Zaria, na hori kowannenku da biyan Tara na tabar kudi N ko daurin shekara dai – dai a gidan Yari.

Ko Tara na N10,000 tare da dauri na watani (6) a gidan Yari.

Kai kuma Matahumi na (4) na horeka da biyan Tara kudi N ko shkara daya a gidan Yari.

Sanarwan Appeal:

Maikara ko Wanda akai kara, wadda bai yardaba, yana da daman ya daukaka kara zuwa gaba, cikin kwanaki Talatin (30 days) daga yau 10/07/17.

(SGD) ( AMINU SA'ADU ZARIA)
THE HON JUDGE
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA ZARIA

CERTISFY TRUE COPY BY:-

(SAMA'ILA MOHAMMED) (ESQ)
ASST.CHIEF REGISTRAR
SHARIA COURT NO.I
TUDUN WADA, ZARIA.

**الملحق ز**: القضية رقم C/No.008/16



Court cikin kwanaki talatin (30days) daga yau 15/02/16.

Aminu S.
15/02/16

S/No. 19/16 — C/No. 008/16
S/Kotu — Sharia court I T/wada, Zaria
M/Sharia — Aminu Sa'adu Zaria.
M/Kara — C.O.P. KDS.
Mat. Mustapha Haruna S/Gari, Zaria
D/Kara — Shiga na laifi da Sata Sect. 174 & 189 SPC
Mai Gabatarwa — Cpl, Adamu Yahaya
R/Sharia — 19/02/16

Jawabin Mai Kara

Amadadin C.O.P. na jihar Kaduna ni Mai No. 252850, Cpl, Adamu Yahaya Ina gabatar da Mat. Mustapha Haruna abisa kan cewa ranar 17/02/16, da misalin karfe 8:00am wani Mai Suna Kamaluddeen Aliyu, Mazaunin S/Layi T/wada yazo ofishin 'Yan Sanda na nan T/wada inda yayi karar cewa wani Mai Suna Mustapha Haruna, Mazaunin S/Gari Zaria, cewa a wannan rana shi Mat. Yayi Masa shiga ta laifi a Dakin Sa Inda ya dauke Masa waya Tecno, Mai Kimar ₦4,500. ao ya kuma dauke masa

waya kirar Nokia, mai kimar N1,500=
Sai karamar jaka mai dauke da
18 card na wurin dikin mkasa
di A.T.M (2) da katin Jabe, a
yayin da aka kama shi mat. an-
Sameshi da waya kiran Tecno,
wadda Mallakine na mkasa, Inda
ya dauka babu izini, Yan haka,
laifine da ya sabama dsarin
laifuka da hukumcin su najihar
kaduna SPC. wannan shine
bayanimmu.

K/G/ Mat.

T.C Mustapha Haruna kaji tuhumar
da ake maka, ka gane, ka yarda
ka amsa laifinka, ko kana da ja?

A: Mustapha yace 1: naji na gane, kuma
rankai dade na amsa.

K/G/ Pros.

T.C cpl, kaji Mat. ya amsa laifinsa,
dud da haka, kana da sheda, ko kun-
gamsu da ikirarinsa?

A: cpl, yace 1: muna da sheda, amma
tunda ya amsa, bamu da wani bu-
katar mu gabatar da sheda akai,
dama yana musu ne, sai mugabatar
da shedummu.

Samu da laifi

Bisa ikirarin da Mat. yayi agaban

Kotu, ba tare da yin tsir sasashi ba,
Kotu ta same shi da laifi ne shiga
ta laifi da sata akarkashin sashi
na 174 da 132 spc. Don haka, Kotu
zata yanke maka hukunci.

K/Q/ Mat.

T/C Kafin Kotu tayi maka hukunci, ko
kana da roko da zaikayi ma Kotu
da zaisa tayi maka Sauki?

A. Mat yace: ie ey akwai, nafarko
dai Ina da Sanaia ba zaman banza nake
yiba, kuma nayi al-kawarin bazan
sake daukan kayan wanibe, Ina zaune
agarin nan akarkashin Malam yahaya,
(kakana ne) Jamaa ya rasu, daganan
nema na kama Sanaiar Lura baro, sai
kuma na koma Sanaiar Shoe Shainer
(wankin takalma) kuma mahaifiyata
ta rasu, ni nake nemamma kaina
Abinci wannan shi ne rokona.

K/Q/ Pros.

T/C cpl, Adamu, kayi rokonsa, kafin Kotu
tayi laiakari da rokonsa, ko kuntaba
samunsa da laifi makamancin haka?

A. Pros. yace: bamu taba samunsa ba,
sai dai akwai alamun ya saba
sai dai abinda Kotu kuma tayi.

Horo

Bisa laiakari da rokon da kayi ma

Kafa na fayi maka Sauki, da kwarin da kayi agaban kotu, ba faye da ka wahalar da Sharia ba, ni Mai Sharia Aminu Saadu Zaria, na horeka kai Mustapha Haruna da biyan taza na kudi ₦3,500.00k daurin watanni uku(3) agidan yari, kuma zaka biya diyyar waya kiran NOKIA ₦1,500.00. Jimila zaka biya ₦5,000.00 kenan.

SHARIA COURT JUDGE
19/02/16
Tudun Wada, Zaria

S/No. 21/16 — C/No. 009/16
S/Kotu — Sharia Court T/wada, Zaria
Mai Sharia — Aminu Saadu Zaria
M/Kara — Abbas Muhd Zaria city
W/Kara — Surajo Garba Izala / Barr. Mon. Lahuga D.I Usman
D/Kara — Zamba da cuta Sections 160 $ 170 SPC
K/Kara — D.C. R/No.
R/Sharia — 26/02/16

Jawabin M/Kara

Tja Abbas mene karanka?

A — Yace: karana shi ne, Ina karan Surajo ne akan ya saida mani da Comp. Mara kyau, akan ₦43,000.00 na sami fana da matsala na dawo masa dashi, yashi ya dade ba kudina ba comp.

Kafu ta kada belinsa Bisa sharud-
da kamar haka:

(1) Mai beli dole ne ya kasance yana
zaune ne a inda mai yake, kuma
ba mai yawan tafiye tafiye ba.

(2) Kuma dole ne ya ajiye Isabar
kudi ₦25,000.00 tare da mashin
rober rober kirar jincheng, kuma
Sabuwa, ko fili a Nagoyi Mai fasawo
da fadin 100X50.

11/08/16

S/No. C/No. 71/2016

S/Kotu - Sharia court 1 T/wada, Zaria

M/Sharia - Aminu Saadu Zaria

M/Kara - C.O.P. KDS.

W/Kara - Idris Abubakar

M/Gabatar da Kara - Sgt Adamu Yahaya

S/Kara - Shiga na laifi da sata Sections
118 da 139 SPC.

R/Sharia - 12/08/2016

Jawabin Mai gabatarwa

A ranar 11/08/16, da misalin karfe
10:45 na safe, wani Mai suna Suleman
Ademola da Simon Maria energi, sun
zo ataze charge office na T/wada inda
sukayi karan ce was a wannan sama

da Misalin Karfe 9:00 na Safe, Mai Suna Idris Abubakar, Bongazzau, sarin ya shigam masu gida ba tare da izininsuba ya sace masu kayayyaki kamar haka:-

ⓐ Generator Modern Sohu tiger, 2700 Mai launin kore, Mai kimar ₦50,000=

ⓑ Gas Cooker, Mai kalan lemu, Mai kimar ₦8,500.00

ⓒ Riguna (3) Masu kima ₦8,000.00

Jimla kimar ya kama ₦66,500.00

a yayin bencikken yar sanda, an Samu Mat. da duk kanin kayan da aka lissafa, yin haka, laifi ne da ya sabama tsarin laifuka da hukuncin su na jihar kaduna a karkashin sashi na 118 da na 139 SPC.

K/G/ Mat.

Tja. Idris kaji tuhumar da aka maka, ka gane, ka yarda haka ne?

A. Idris yace i naji na gane, kuma na yarda haka ne, na amsa.

K/G/ Pros.

Tja. Pros. kaji Mat. yace i yaji ya gane kuma ya amsa laifinsa, me kace?

A. Pros. yace cci muna rokon kotu da tayi masa hukunci a takaice (Wato Summary trial).

Samu da laifi

Bisa ikirari da kayi agaban kot na jinsa laifin da ake tuhumarka akai, na shiga na laifi da yin sata, na sameka da laifi wadda janyi maka hukumci a fakaice.

Roko ko Hanzari

T/c K/G/ Mat. Idris kana da roko da zakayima kotu wadda zatayi la'akari dashi tayi maka sassauci wajan hukumci?

A Idris yace: "Ina dashi Sabode dallai nasan na jinsa laifina don haka, ina roko kotu tayi mani sauki, dasu kamsu wadanda naiyima Satan.

K/G/ Pros.

T/c Sagent, kaji rokon mat. ko kana da masaniya akan halin shi mat

A Sgent yace: "wannan shine karo na farko aguzinmu!

Horo

Bisa la'akari da rokon da kayima kotu, da bayanin da pros. yayi agaban kotu game da cewa: bai San halinka aba, wannan shine na farko aguzinsu. kotu ta hore ka kai Idris da biyan tara

na jimlar kudi ₦10,000.00 ko watanni (6 months) agidan yari. Kuma zaka biya Diyyan wahal-halun kaiwa da komowa na kudi ₦2,000.00.

Daman Appeal

M/Kara ko W/Kara, wadda bai yardaba, yana da daman ya daukaka kara zuwa gaba, cikin kwanaki talatin (30 days) daga yau 12/08/2016.

SHARIA COURT JUDGE, Sign. Date 12/08/16, Gudun Wada, Zaria

15/08/16

Daga Shafi na (233) C/No 64/16

C.O.P. Vs: Fatima Muhammad

Yau kafu ta dawo don cigaba, kuma dama kafu tasa yau ne zata cigaba

K/G/ Mai gabatar da kara

T/C Sgt. Me ake ciki bisa kan wannan Sharia?

A Sgt. Yace: Suna Adamu Yahaya, tare dani akwai lawyer mai Saido Aisha Ahmad da Khadija Ibrahim. In kafu bata Mantaba, Mat. an a tuhumar ta ne abisa kan jawo Sanadin jin rauni, ta hanyar Qasfuri

63

Court cikin kwanaki talatin (30 days) daga yau 15/02/16.

[signature] 15/02/16

S/No. 19/16 — C/No. 008/16
S/Kotu — Sharia court I T/wada, Zaria
M/Sharia — Aminu Sa'adu Zaria.
M/Kara — C.O.P. KDS.
Mat. Mustapha Haruna S/Gari, Zaria
D/Kara — shiga na laifi da sata sect. 174 & 189 spc
Mai Gabatarwa — cpl, Adamu Yahaya
R/Sharia — 19/02/16
Jawabin Mai Kara
Amadadin C.O.P. na jihar Kaduna ni Mai No. 252850, cpl, Adamu Yahaya ina gabatar da Mat. Mustapha Haruna abisa kan cewa ranar 17/02/16, da misalin karfe 8:00am wani Mai Suna Kamaluddeen Aliyu, Mazaunin S/layi T/wada yazo ofishin 'Yan Sanda na nan T/wada, inda yayi karan cewa wani Mai Suna Mustapha Haruna, Mazauni S/Gari Zaria, cewa a wannan rana shi Mat. yayi masa shiga ta laifi a Sakin S... inda ya dauke masa waya Tecno, Mai Kimar ₦4,500 ao ya kuma dauke masa

٢٥٧

Samu da laifi

Bisa ikirari da ƙaiji agaban Kat
na jinsa laifin da aka tuhumata
akai, na shiga na laifi da
yin sata, na samaka da laifi
wadda jangi maka hukumai
afakaice.

Roko ko Hangari

T/c K/Gl Mat. Idris kana da
roko da zakayima kotu wadda
zatayi la'akari dashi tayi
maka sassauci wajan hukumai?

A Idris yace: "Ina dashi saboda
Allai nasan na jinsa laifina
don haka, Ina roko kotu tayi
mani sauki, dasu kansu wadan-
da nayima satan."

K/G/Pros.

T/c Sagent, kaji rokon mat. ko kana
da masaniya akan halin shi mat.

A Sgent yace: "wannan shine
karo na farko aguzinmu!"

Horo

Bisa la'akari da rokon da kayi
ma kotu, da bayanin da pros. yayi
agaban kotu game da ce wai bai
san halinkaba, wannan shine
na farko aguzinsu. Kotu ta horo
ka kai Idris da biyan tara